# EPISODE ONE

**SALIS.** Kai amma fa wannan lamari sam ba dadi ganin yadda canjin yanayi ke yiwa harkar noma illa a nan.

Gaba daya baka iya has ashen me ka iya faruwa ba a irin wannan yanayin, kuma hakan na iya kawo illa ga yabanya ko amfanin gona

**RABI.** Hmm wannan lamari ai sai dai addu'a kawai wannan Magana fa haka take

Cikn yan shekarun nan fa ana fadi – tashi ne kawai a harkar noma, ruwan

Sama fa yayi karanci a wurare da dama, sannan idan ruwan ya samu ko dai ya zamo mai yawan gaske da ka iya lalata amfanin gona, ko kuma yayi karanci wand aba zai ishi yabanya ba, abu ya zama kila- wa kala musamman idan zamuyi shuka muna dar-dar da irin yanayin

**SALISU** Kinga ko hakan zai yi mutukar shafar yalwar amfanin gona da za'a iya samu.

**RABI** Maganar ka dutse, hakika haka abun yake kaga yanzu fa irin yabanyar dake samar da dinbin amfanin gona da kyar suke kai labara, sannan kuma kwari da tsutsotsi sai karuwa suke suna damun yabanya sabida wannan canjin

na yanayi.

**SALISU** Hakane Rabi, kuma na lura yanyin zafi ma fa karuwa yake.

**RABI** Kwarai da gaske kuwa, zafi yana nema ya gagari kundila, kuma ka ga yabanya irin ta masara, da shinkafa suna da irin adadin zafin da zafin da suke rayuwa dashi a lokacin da yabanyarsu ke girma, idan aka samu akasi sai kaga ba'a sami komi ba  a noman masara ko shinkafa sabida yanayin zafi.

**SALIS** Shin irin wannan idan yana faruwa akwai wata hanya na kaucewa yanayin don gudun asara ko ince mafita ?

**RABI** Hkika mun fara gwada shuka wadansu iri wadanda zafi baya musu lahani , wadanna irin suna nan daban-daban ,Amma fa suna da tsada a gidan gona ba kamar wadanda muka saba siye ba ,haka kuma zai kasance akwai dan kalubale wajen fara amfani da irin wannan ga kananan manoma irina.

**Salis.** Abin takaici a nan shine wadanda ke taimakawa wajen ganin cewa yanayi ya daidaita su suke shan wahalar

Interlude wakar noma

Rabi batun ruwa fa ?, shin ya kuke tattala ruwa don aikin noma?

**RABI.** Gaskiya fa karancin ruwa ya fara zama abin damuwa, ka ga dai rafika da kogi ke samar da isashhen ruwa a ko da yaushe sai bushewa suke musamman a wannan shekarar.

**SALIS** Subahanallahi Allah gamu gareka …. Barawo a hannun mata canjin yanayi irin wannan na saukar ruwan sama na shafar dabbobi suma ko Rabi?

**Rabi** Fadi ka kara Salis wannan haka yake .

**Salis** Wannan irin yanayifa ana toshe wannan matsala ne wata matsalar na kunno kai a harkar noma, wadanda kuma fa hakan na shafar rayuwar muu mutuka da samar da abinci ga al'umma.

Shin kinga wata gwamnati a wani mataki na kokarin kawo dauki a wannan lamarin kuwa ?

**RABI** akwai tsare – tsare da gwamnati tayi, amma, a gaskiyar lamari suna kawai dan ba'a aiwatar da su ba, Muna so mu gani a zahiri abinda gwamnati ka iya yi misai yana da kyau gwamnati ta bawa manoma horo na musamman kan dumamar yanay, da dabarun aikin gona na zamani ta yanda zasu amfana ga noma na kimiyya da fasaha.

**SALIS** lallai a zahiri yake hakkin magance matsalar dumamar yanayi ya rataya a wuyan kowa, don haka yana bukatar hanyoyin magance shi da dama, don

samun yiwuwar aikin gona mai dorewa sannan da samun kyawawan tsare-tsare na tattalin ruwa don taimakawa kananan manoma, sannan dole a wayarwa mutane kai akan rage

**EISODE TWO**

**MERO** Iyabo kwana biyu kamar bakya kauyen nan, shin ya canjin yanayi ke shafar rayuwarku ta fannin tsaftar muhalli da samun ruwan sa me tsafta?

Kinga dai rafika a yan shekarun nan bushewa suke, idan ruwan sama ya zo kuma a samu ambaliya wanda kan gurbata ruwan rijiya da sauransu, shin ya kuke yi?

**IYABO** Toh! Alhmadulillahi, amma gaskiya muna shan wahala, ba sauki don sai mun je wurare mai nisa a kafa muke samun ruwan sha, kuma ruwan ba kyau mutum ya sha.

**MERO** Wato bama karancin ruwa ne kadai matsalar kuba hada matsalar ruwa marar tsafta kenan?

**IYABO** Sosai kuwa kinga sabida canjin yanayi duk hanyoyin samun ruwan mu basa Samar mana da ruwan, kuma rijiyoyin mu duk sun kafe, rafi sun bushe, sannan muhallin mu ya gurbace wannan bala'I ne fa

**MERO** Akwai wani abu da kuke yi ne kawo yanzu don shawo Kan matsalar lamarin da kuma samun saukin tafiya da wannan yanayi?

**IYABO** muna kokarin yin haka ta hanyar ajiye tankuna da manyan randar Tara ruwa don Tara ruwan Sama, amma kudin sayen wadannan abubuwa fa da kulawa da su sun fi karfin mutane da yawa a wannan kauyen.

**MERO** Da alama kuna da bukatar taimakon gwamnati da kasashen ketare don showo Kan wannan matsala.

**IYABO** Wannan haka yake, muna bukatar kudi da kwararru a fannin tsafatace ruwa da kuma muhalli Wanda shima wani matsalar ne mai zaman kansh.

**MERO** Wadansu kalu-bale kuke fuskanta ta bangaren tsaftace muhalli?

**IYABO** Kinga dai sabida karancin ruwa ko'ina bola ta cika, masai ma sun cika idan akayi ruwan sama sosai duk za su bi hanyoyin ruwan da muke sha su gurbata su wanda hakan ke haifar da ciwon Kwalara.

Muna bukatar sabon tsari da zai magance wannan lamari

**MERO** Lalle wannan Babbar matsala ce, Akwai wani abu da gwamnati ke yi kuwa?

**IYABO** Toh! Gwamnati ta fara wani abu amma ba ta da tsari mai kyau, Muna so a magance wannan matsaloli.

**MERO** Hakika kuna bukatar ayyukan sa kai, shin mutanen wannan kauyen sun san cewa duk wadannan matsaloli daga canjin yanayi ne?

**IYABO** Eh toh da yanmu dai neman abincin da zamu ci yau da gobe kawai muuka sanya gaba dan mu rayu, muna bukatar ilimin abin a wayar mana da kai don sanin cewa muke haddasa canjin yanayi da gurbata muhalli.

**MERO** Gaskiya ne, matsalar canjin yanayi duk duniya ne, amma dole ne muyi wani abu don magance wannan matsala musamman a irin wannan kauyen Naku.

**IYABO** Hmm Kalamanki sun faranta min rai Mero na sami karfin gwuiwa cewa zamu sami mafita da taimakon mutane irin Ki

**MERO** Zamu hada karfi da kafe domin wayarwa da mutane kai kan abubuwan da muke yi da ke haifar da canjin yanayi da guratar muhalli, sannan da hanyoyin samun mafita.

**EPISODE THREE**

**SANI** Jamila ko kin lura da yanda yanayin damina ya canja gaba daya a yan shekarun nan?, shekarun baya mukanyi has ashen saukar ruwa da kuma sauransu, amma yanzu sai yadda ka ga ruwa kawai.

**JAMILA** Wanna n gaskiya ne Sani, canjin yanayi ya riskemu dole mu nemi hayoyin rayuwa a cikinsa. Kasan iyaye da kakanninmu suna da ilimin yanayi irin namu na gargajiya kuma haka suka rayu ba tare da wata matsala ba.

**SANI** Kika ce ilimin yanayi irin namu na gargajiya ? Dan karamin haske mana.

**JAMILA** Kwarai da gaske kuwa, ilimin namu na gargajiya iliimine na baiwa da basira da Allah ya baiwa iyaye da kakanninm, muna lakantar yanayin damina, rani, bazara da yanayyin hunturu da sauransu. Sannan kuma a wadannan lokutan sun san yanayin da zasu yi shuka, cirbe da girbi da kuma sauuransu.

**SANI** Toh amma yanzu da aka sami ci gaba irin na kmiyyya da fasaha irin wannan ilimin nasu na tasiri kuwa ?

**JAMIILA** Kwairai kuwa ! kakaninmu basu a na’urori irin na kimiyya da fasaha amma sabida baiwa da Allah yayi musu da kuma bin yanayi sau da kafa ya sanaya suka san ko wani irin yanayi da riga kafi idan suka hango wani bala’I irin na ambaiya ko kamfar ruwa.

**SANI** **I**allai wannan baiwa ce daga Allah, to ya kke gani za’a yi don tabbatar da kasancewar wannan ilimi na gargajiya ba tare da ya bace ba

**JAMILA** gaskiya wannan wani kalubale ne, amma dole ne muu diinga kasancewa tare da manyan mu muna koyon wadannan abubawa daga gare su muma mu koyawa yaran mu da jikoki.

**JAMILA** A nan zan iya cewa da farko noman abubuwa daban-daban irin wadanda iyaye da kakanni keyi a da can hakan na maganiin yanayi irin wanda ya daburce wanda ba'a iya hasashenshi

**SANI** **N**a jinjina miki, ta ya za'a iya janyo hankalin matasa don su rungumi wannan ilimin sannan su rinka amfani da shi?

**JAMILA** Ilimi ko wane iri ne yana da mutukar amfani, kamata yayi makarntu su sanya irin wannan ilimi a manhajarsu a dinga koyawa matasa, sai taruka na kara wa juna sani da sauransu.

**SANI** Hakika ilimi gishirin zaman duniya ne, kina gay a dace gwamnati ta sanya ilimi gargajita irin wannan a cikin tsare-tsarenta ?

**JAMILA** Kwarai kuwa, yana da kyau gwamnati ta dauki ilimi irin wannan ta sanya cikin tsare-tsarenta wannan mai martaba ala'dun mu ne.

**SANI** Lokaci yayi da zamu rungumi ilimin gargajya na yanayi domin samun ci gaba

**JAMILA** Naji dadin wannan tatttaunawa ta mu lokaci yayi da zamu hada hannu don magance matsalar canjin yanayi da ke damiun mu

## EPISODE FOUR

**RABI** Yanzu dai kam a zahiri yake yanayi ya canja ruwan sama baya sauka yadda akka saba gani a shekarun baya, wanda hakan na yi wa harkar noma illa da rayuwar mu.

**JAMILA** Wannan haka yake, kuma abu ne wand aba zamuyi wasa da shi ba. Iyaye da kakanninmu allah yah ore ma su ilimin lakantar yanayi ko wane iri, kuma duk yanda ya canja suna da basira da ilimin tafiyar dashi.

**RABI** Ilimin gargajiya na yanayi da muhalli kika ce fa, kamar yaya karamin haske kan batun mana.

**JAMILA** Kwarai kuwa, Allah ya baiwa tsaffin mu baiwar sanin yanayi dabn-daban, sun lakanci yanda kasar noma take, da halayyar dabbobi da tsirrai da sauransu, wannan ilimi da suke da shi yana mutukar taimaka musu a harakar noma .

**RABI** Lallai wannan abin mamaki ne kuma abin sha'awa, to amma a wannan zamanin na kimiyya da fasaha wannan ilimi nasu zai yi tasiri kuwa?

**JAMILA** Kwarai da gaske kuwa zai yi tasiri fiye da yadda kike tsaammani, su kam bsu da na'urori amma suna da basira ba kadan ba, a don haka akwai abubuwan da zamu koya daga garesu.

**RABI** Hakika na gamsu , to amma ta yaya zamu tabbbatar dda cewa wannan iliimi nasuu bai bace ba bat daga doron kasa ba?

**JAMILA** Wannan tamabaya ce mai ma'ana da muhimmanci, dole ne mu dinga kasanacewa da manyan mu tsaffi a ko da yaushe, kuma mu dinga koya daga garesu, idan ma ya kama a dinga yin bidiyyon dinsu ana adanawa .

**RABI** Jamila ta yaya kike ganin cewa ilimin gargajiya na iyaye da kakanni akan yanayi da muhalli zai iya maganin canjin yanayi

**JAMILA** Ki fara duba yanda kakanninmu a da can ke samar da wuraren adana ruwa da damina don amfani da shi wajen noman rani ko kuma lokacin kamfan ruwa, kinga yin haka ai tattalin ruwa ne don magance matsalar yanayi saukar ruwan sama.

**RABI** Kai lallai wannan batun naki gaskiya ne, to amma ya zamu janyo hankulan matasa don su fahimci muhimmancin wannan ilimi na iyaye da kakanni?

**JAMILA** Ilimi dai gishiri zaman duniya ne, yana da kyau makarantn ilimi su sanya wannan a cikin manhajar karatunsu don karantar da matasan mu, sannan da shirya tarukan kara wa juna sani da wuraren sha'ani da sauransu.

**RABI** Masha Allah, shin kina gani akwai bukatar shigar da wannan muhimmin ilimi a cikin tsare-tsaren gwamnati don aiwatarwa?

**JAMILA** Sosaima kuwa yana da kyau a sanya ilimin iyaye da kakannimu na gargajiya a cikin sabbin tsare –tsare don nunawa matasa darajarsa da amfaninsa.

**RABI** Jamila ko shakka babu kin wayar min da kai, sannan na fahimcin cewa ilimin gargajiya akan yanayi na iyaye da kakanninmu zai yi tasiri mutuka wajen magance matsalar canjin yanayi

**JAMILA** Idan har muka darajar iriin rayuwar tsaffinmu na baya da irin baiwar da allah ya basu zamu maganin matsalolin nan.

**RABI** Gaskiya na karu sosai

**JAMILA** Naji dadin fahimtar cewa kin koyi wani abu a yau, kuma kinga zamu iya gauraya ilimin kakanninmu da na zamani mu nuna wa duniya cewa muu kaifi biyu ne, kuma zamu iya dogaro da kanmu a nan gaba

## EPISODE FIVE

**SALIS** Shin kin lura da irin yanayin da muke ciki a halin yanzu wanda aba ma iya gane lokacin saukar ruwa da zuwan sanyi ko zafi da sauransu? Abin fa sai kara rikicewa yakeyi don yana da mutukar wahala mutum ya iya has ashen yanayi kamar yanda muka saba yi a shekarun baya.

**RABI** Wannan haka yake salis kuma kaga chanjin yanyin da aka samu yana iya yiwa muhallinmu illa da mu kanmu gaba daya , amma fa kasan cewa iyaye da kakanni na da baiwar sanin yanda yanayi ke juyawa yadda su kan chanja idan yanayi ya chanja allah ya basu ilimin abin.

**SALIS** Kina nufin ilimin hasashen yanayi na gargajiya da iyayenmu ke amfani da shi? Ina yawan jin wannan fad an Allah kara min bayani akan irin wannan baiwar da Allah yayi musu

**RABI** Babu shakka allah ya yiwa iyaye da kakannimu baiwar sanin yanayi ko wani iri, suna bin yanayi sau da kafa, sannan suna amfani da shi yanda ya kamata.

Sun san yanda kasar noma ta ke,da ruwa da yabanya ko wace iri a haka suka rayu na tsawon lokaci.

**SALIS** Kai lalle suna da basira, to amma ba kya ganin cewa zuwan kimiyya da fasaha da Nau'rorin zamani irin nasu ilimin zai zama tsohon yayi har ma ya bace bat?

**RABI** Ko kadan, ni zan iya ce maka ma wannan ilimin sauyin yanayin wanda kakaninmu suke da shi yafi tasiri, sabida duk yanda yanayi ya chanja masu su kuma su na da yadda suke bullo masa don tafiya dai-dai da yanayin a tare da wata matsala ba. Kaga sukan tanadi wuraren adana ruwa a lokacin damina da zarar an sami karancin ruwa na wani lokaci sai su yi amfani da ruwan da suka tara a gona ga yabanyar da ba ta jure zafi da rahin ruwa.

**SALI** Kai amma fan a karu da wannan da wannan bayani naki, amma abin tambya a nan shine, ya kike ganin zamu iya kula da wannan ilimin na kakanninmu harma yara da jikokin mu su amfana da shi ?

**RABI** Yin aiki tare na da muhimmanci ga al'ummar gari, sannan a girmama al'adunmu na gargajiya.

Bayan haka a sanya wannan ilimi a cikin tsare- tsaren mu na kasa kuma a aiwatar da su, idan aka yi haka har maganin chanjin yanayin da muke fama da shi za'ayi

**SALIS** Naji dadin wannan bayanu naki Rabi, shin rabi akwai wani misali na inda irin wannan ilimi na kakaninmu yayi tasiri ?

**RABI** Ga misali nan kana gani karara na gandun dazuzzuka da muke da su inda suka dasa itatuwa. Don maganin yanayi na iska wadanda kuma ke iya tsotse sinadarin carbon dioxide kuma ya rage illar chanjin yanayi

**SALIS** Rabi ta ya za mu wayar wa da jama'a kai akan muhimmanci wannan baiwa na yanayi da Allah yayiwa kakanin mu?

**RABI** Ilimi d ai gishiri zaman duniya, ya kamata mu hada hannu ne da makarantun da ke cikin garuruwan, mu da majalissun mu sannan a sanya wannan ilimi cikin manhajar makarantun don koyar da yaranmu.

**SALIS** Gaskiya na hango mafita cikin wannan lamari amma sai mun chanja irin tunaninmu ko bah aka ba?

**RABI** Wannan haka yake, kawai sai mun yarda da cewa kakannin mu sun yi amfani da dukkan yanayin da ya riskesu kuma sun gama lafiya ba tare dda wasuu matsaloli ba

***SALIS*** Na gode mutuka da wannan haske da kika karamin, na sami kwarin gwuiwa.

**RABI** Ba komi salis, za mu gudu tare mu tsira tare kan wannan lamarin, kuma zamu hada ilimiin zamani da na iyaye da kakannin mu don magance matsalolin chanjin yanayi da tsaftataccen muhalli kona gawayi a fadin duniya.

**RABI** Hmm hakika wannan gaskiya ne

**SALIS** Wannan aikin ne babba, amma, tattaunawa irin wannan, yana karami kwarin gwuiwar cewa zamu iya samun chanji duk da irin kalubalen da ke tunkarar mu daban-daban

**EPISODE SIX**

**SALIs** Jama'a barakanmu da warhaka, ina ma kowa barka da zuwa da halartar wannan wuri. A yau ina so mu tattauna akan yadda gurbatar yanayi da muhalli da yadda zamu magance lamarin ta hanyar dawo da kimar muhallinmu da yanayi

**RABI** gaskiya ne Salis hakika ya kamata musan yanda gurbacewar yanayi ke yimin Allah da muhallinmu sannan da sanin cewa lallai hakika gurbacewar muhallin mu na yi mana illa kuma mu ke taimakawa da wani kaso wajen gurbata muhalli da yanayin mu wato (CLIMATE JUSTICE).

**SHEHU** Wannan haka yake Rabi, yakamata mu fahimci haka sannan mu san ta yadda zamu bullowa lamarin don magance illar gurbacewar yanayi da muhallin mu ta hanyar amfani da sabbin dabarun hanyoyin samun haske da makamashi wato renewable energy

**JAMILA** Na yarda da wannan batun naka shehu komawa ga samun hasken wuta ta amfani da hasken rana wato Solar da amfani da iska, da ruwa zai rage dumamar yanayi sosai wanda shi ke haifar da chanjin yanayi

**SALIS** To amma fa yakamata mu duba yanayin yanda tsadar abin yake idan muka ce muna so mu dinga samun hasken wuta da maka mashi ta wadannan sabbiin tsarin,shin ta yaya talaka zai mallaki wannan sabon hanya wato renewable energy ba tare da aljihunsa ya koka ba wannan shine abin tambaya.

**RABI** Gaskiya da wannan dan wannan fa, indai ana bukatar haka to fa sai anyi wa talaka tallafi, na samun wadannan abubuwa sannana a tsari me kyau ga masu karamin karfi ta yadda zasu iya sa kudi su siya duk wani abu da zai taimaka don samun hasken lantarki da maka mashi a kudi mai rahusa

**SHEHU** Ance dai me daki shi yasan inda yake masa yoyo, Mutanen gari su zamo masu zama su tattauna matsalolinsu sannan su yanke shawarar abin da zai taimakesu,wanda hakan zai sanya su samar da wuraren da mutane zasuyi aiki da sauransu

**JAMILA** Samar da hasken lantarki ta hanyar hasken rana hanyace me dorewa yakan dade duk da cewa da farko akwai kasha kudi, amma yafi dayan hanyar samar da haske ta hanyar man fetur

**SALIS** Wannan haka yake  Jamila, to yaya duniya ke kallon wannan sabon hanya ta samar da hasken lantarki, sannan ta yaya zai rage dumamar yanayi da muhallin mu?

**RABI** A gaskiya wannan hanya na rage yawan zafi ta hanyar rashin haifar da gas idan ka kwatanta ta hanyar amfani da man fetur wanda ke haifar da zafi

**SHEHU** Ai bama wannan kawai ba komawa ga sabon tsarin yana rage gurbacewar iska wanda ke cutaway lafiyar mu

**JAMILA** Kuma hasken solar da na iska na dadewa sosai ba kamar na'urar generator ba da sauransu

**SALIS** Yanzu dai a zahiri yake  hanyoyin samar da hasken lantarki da maka mashi na zamani sune mfita ga dumamar yanayi, amma ta yaya ta yaya zamu magance kalubalen da ke tattare da komawa ga wannan sabon hanyar?

**RABI** Shi dai kawata gari abu ne mai kyau yakamata gwamnati da kamfanoni masu zaman kansu su koma ga wannan hanyar da samar da wuraren dake chaza abubuwan da ke amfani da wutar lantarki, sa'annan su rarraba wadannan kaya ga Al'umma.

**SALIS** Hada kai da kasashen ketare da suka ci gaba zai taimaka kwarai wajen smun tallafi da koyar da mutane yadda abin yake

**EPISODE SEVEN**

**SALIS** Lale marhabin ina yiwa kowa barka da zuwa wannan wuri don tattauna muhimman batutuwan da suka damemu musamman dumamar yanayi da sauransu. Sunana Salis kwararre a bangaren muhalli, zan kasance tare da ku a wannan tattaunawa allah yaasa mu kasanace tare da ku a wannan tattaunawa, Allah yasa mu kammala lafiya.

**RABI** Jama'a barkanmu da warhaka sunana Rabi yar gwagawarmayar samarwa mutane sauki, Da farko dai dumamar alkarya shine zafi ko dumi da birni ko alakarya ke dauka wanda yafi na kauyuka da ke zagaye da shi sabida hada-hadar arayuwa da yawan mutane da ke cikin birane da gine-gine da ababan hawa da sauransu.

Irin wadannan birane babu shuke-shuke na itatuwa, lambuna ko dazuka wanda hakan ke shafar mutane ta fannin kiwon lafiya.

**SHEHU** Haka ne Rabi, A matsayina na kwararre ta fannin tsara birane kankare da dakali irin na tsakiya da gefen tituna na daukar zafi kuma su dumama gari wanda hakan na kara mizanin zafi

**JAMILA** Ina yi wa kowa lale marhabin, sunana Jamila mazauniyar wannan gari na lura dda cewa makwabtanmu bassu da itatuwa , ba su da wuraren shakatawa wato (park). Ya suke ji lokacin zafi?

Sannan ya shuke-shuke da tsirrai ke taimakawa wajen rage zafi?

**SALIS** Wannan tambaya ce me muhimmanci,hakika itatuwa da tsirrai da wuraren shakatawa da ke cike da shukar fulawoyi da ciyayi da itatuwa suna taimakawa sosai wajen rage zafi a lokacin zafi, suna bada lafiyayyar iska kenan.

Dole ne mu tabbabtar da cewa ko ina ya kasance green wato kore don sanyaya wuri da kuma samun iska mai kyau.

**RABI** Wannan haka yake, in ji Bature ya ce Climate Justice wanda ya kamata a ce ko ina ya kasance kore wato ya kasance da itatuwa fulawoyi da sauransu, ba tare da duba irin arzikinsu ba ko kabilar sub a.

**SHEHU** Rabi wannan batu haka yake a matsayina kwararre a fannin tsara birane, akwai yiwuwar mu yi aiki kafada -da kafada don sanin bukatunsu.

**JAMILA** Ina son wannan batun na shuka itatuwa da yin wuraren shakatawa me cike da shuke-shuke. Amma ta yaya zamu sami kudin yin wannan aikin?

**SALIS** Gaskiya kudi ne muhimmi a cikin wannan batu

**JAMILA** Akwai hanyoyin samun kudi, gwamnati zata iya yin Budget din wannan wato kasafi don a samar da wannan, sannan mutane su goyi bayan kawo wannan sabon hanyar kawo wutar lantarki sai kuma hukumomi masu zaman kansu suma za su iya bada rancen kudade.

**RABI** Sannan fa kada a manta cewa gina wuraren shakatawa da sauransu zai samar da guraben ayyuka ga matasa, kun ga ko haka zai taimakawa muhallinmu da tattalin arzikin mu.

**SHEHU** Bayan haka za'a dade ana morar irin wannan ci gaba na samar da muhalli irin na ko ina kore inda itatuwa suke da wuraren shakatawa, hakan kuma ba shakka zai rage shan AC wato na'urar sanyaya wuri wanda kan haifar da cututtuka da kuma zafi da ke fita na jikin Na'ura ya dumma yanayi. Kenan koren muhalli na samar da iska mai lafiya sosai

**JAMILA** Ta ya zamu tabbatar da cewa wannan sabon hanyar magance dumamar yanayi be yi wa mutanen da ya kamata su taimaka a cikin lamarin ill aba?

**SALIS** Da wannan don wannan, kin sosa min inda yake min kaikai, idan zaa yi irin wannan abu hakika akwai farashin kadarori na karuwa a don haka kwararru ta bangaren tsara birane da masu kawo sabbin tsare-tsare, dole

ne su tabbatar sun samar da gidajen haya da talakawa zasu iya biya sannan da kayyade kudaden haya da sauransu.

**SHEHU** Gaskiya zamu tabbatar da cewa talaka ya samu dukirin wadannan abubuwan more rayuwa ba sai masu hali ba kawai

**EPISODE EIGHT**

**SALIS** Ina mika godiya ta a gare ku duka na jajircewa don halartar dukkan tarukan da mu ke yi musamman wannan. Da haka nake muku lale marhabin barkan mu da sake saduwa.

Da farko dai kamar yadda kuka sani sunana Salis kwararre kuma massani a bangaren muhalli.

Zamu fara tattaunnawar ne yau da batun yadda dumamar yanayiya shafi kowa, kuma yau zamu duba yadda abin ke shafar mutanen da ke zaune kusa da gabar teku ne da manyan koguna.

Rabi ko zaki dan yi mana matashiya akan yadda kowa ya kamata ya zauna a wuajen da yake kore shar cike da itatuwa, da shike –shuken fulawa da tsirrai masu kyawon furanni?

**RABI** Kwarai kuwa Salis kaga dai kamar yadda Bature kan ce Climate Justice mu kuma mukan ce illa ga chanjin yanayi ko daumamar yanayi kanyi ga wadansu mutane wanda hakan kan sanya su rasa wadnsu ababen more rayuwa da tattalin arziki, kai har ma da siyasa da sauransu.

Irin wadannan mutane sun hada da mutanen da ke zaune a kusa da ruwa kogabar teku wadanda ke fuskantar barazanar ambaliyar ruwa. Da rasa rayuka, da rasa matsuguni, kamar yadda zamu tattauna mafita kan lamarin yanada kyau mu fahimci cewa mutanen da ke bada gudunmawa kasancewar dumamar yanayi ba su ke shan wahalar ba.

**IRO** Rabi duk naji maganar da kikayi, a matsayi na na me wakiltar wannan karamar hukuma. Muna sane da irin kalubalen da mazauna gabar ruwa suke fuskanta, sannan ina so in sanar da ku cewa za muyi dukkan mai yiwuwa insha Allahu don ganin cewa mu magance matsalarsu

**RABI** Ga wata can na daga hannu

**SALIS** Jamila Bisimillah, muna jinki

**JAMIILA** Ta yaya za a tabbatar da cewa anyi adalci a matakan da za'a dauka?

Sannan ya zamu aiwatar da dukkan tsarin abubuwan da muka kawo?

**SALIS** Wannan tambaya ce me muhimmanci. Da farko dai zai kasance kofar mu a bude take kuma za'a tafi tare da kowa wajen yanke dukkan wata shawara da za'a yi

Sai kuma hada hannu da za'a yi tsakanin masu ilimin kimiyya da shuwagabanni unguwann, sannan dole mu farfado fa harkar ilimi kuma mu tallafawa mutane ta hanyar sana'a.

**RABI** Sannan kuma kada a manta da muhimmancin yin abubawa da mutane nab akin ruwa ke bukata na more rayuwar yau da kullum, musamman abubuwan more rayuwa da kuma gaya wa mutane cikin lokacin yiwuwar faruwar ambaliya ko dumamar yanayi  da yadda mutane zasu tafi da canjin yanayin.

**IRO** Rabi an gaisheki, wannan batun haka yake, duk da yake duk wadannan abubuwan na bukatar kudi ne to, amma muna yin dukkkan mai yiwuwa dom magance tororkon ruwan teku da ambaliyar ruwa da sauran matsalolin da ake samu a garuruwan dake dab da gabar teku

**RABI** Wannan yayi kyau, muun gode. To wadanda ba za su iya jure tafiya da yanayi b aka iya yin kaura su bar wajen? Kasan dai ba zamu barsu a bay aba

**SALIS** Irin wadannan mutane za mu yi kokarin sama masu aiki ne da wuraren zama a wadanda zasu iya biya sannan da wadansu ababen more rayuwa.

**EPISODE NINE**

**SALIS** Ina yiwa kowa barka da zuwa wannan wuri don mu tattauna, lale marhabin. Da farko dai sunana Salis kwararre a bangaren muhalli da kula da lafiya.

Ba tare da bata lokaci ba mu fara abin da ya tara mu a nan tunda Hassan ya riga ya bude taro da addu'a. Hassan ko zaka iya gaya mana wani abu game da dumamar yanayi ko chanjin yanayi da yadda yake shafar mutane ta fuskar kiwon lafiya?

**HASSAN** Kwarai kuwa, kaga dai da farko mun gane cewa wadansu mutane ko garuruwan mutane kan tagayyara bayan chanjin yanayi mai zafi, da ambaliyar ruwa ko karancin ruwa ko gurbatar iska da muke shaka ko kuma raba mutane da matsuguninsu shi Bature ke kira da "CLIMATE JUSTICE".

Idan aka sami dumamar yanayi ruwan sama ya sauka fiye da kima aka sami ambaliyar yakan gurbata ruwan sha da iska wanda hakan zai iya haifar da cututtuka da akan samu ta ruwa ko ta iska kai harda Vector borne disease da wadansu cututuka da dama. Ya kamata ayi gaggawar shawo kan wannan lamari.

**JUMMAI** Subahanallahi, gaskiya wannan abin damuwa be mutuka, a matsayina ina jin yanda lafiyar yara zata kasance a cikin irin wannan halin.

Ta yaya zamu iya tabbatar da cewar mutanen mu an shirya wa irin wanan bala'in da chanjin yanayi ke haifarwa kafin ya zo?

**SALIS** Wannan tambaya ce mai kyau Jummai, da farko dai malaman lafiya da tsaftar da tsaftar muhalli da ke rayuwa a wannan garin irin su Iyabo za su taimka sosai ta hanyar wayar wa mutane kai na yadda zasu tunkari wannan lamari da nuna musu yadda zasu yi wasu abubuwan da zasu taimaka.

**IYABO** Salis ai duk jirgi daya ya kwasso mu amma tun da nike zaune a wannan garin bari ingaya muku abinda yake kasa.

Bangaren mu na kiwon lafiya na aiki tukuru wajen wayar wa da mutane kai, akan illar chanjin yanayi. Muna hada hannu da makarantu, da kungiyoyi da da kwararru a bangaren kiwon lafiya don samar da mafita, da samar da kayayyakin kiwon lafiya na agaji, da kula dda marasa lafiya da suka jikkata.

**HASSAN** Kai amma hakan yayi kyau, amma akwai bukatar maganin asalin abin da ke haifar da dumamar yanayi don kare lafiyar mu. Ya kamata mu koma ga sabbin hanyoyin samara da hasken wutar lantarki da makamashi.

**JUMMAI** Wannan haka yake Hassan, amman fa akwai batun kalubale na kudi idan zaa koma sabbin hanyoyin. Shin ya zamu tabbatar da cewa nauyin kula da kai be taruwa wadanda matsalolin dumamar yanayi nan ya shafa ba.

**SALIS** Wannan tambaya ce me muhimmanci jummai yana da kyau a kawo sabbin tsare-tsare wadanda bama don su rage faruwar dumamar yanayi ba kadai a'a wadanda zasu kasance babu kara lalata komi ba

**HASSAN** Kada kuma a manta da rawar da bangaren ilimi zai taka wajen karantarwa da wayarwa al'umma kai yadda wannan abu ya shafi kiwon lafiyar mu.

**IYABO** Wannan haka yake, yana da kyau a dinga shirya taron karawa juna sani a da gangamin tsaftace muhalli sannan da yin shakatawa me cike da shuke-shuken itatuwa da fulawa

**EPISODE TEN**

**SALIS** Kai balarabe naji dadin sake haduwa da kai , kaga dai matsalar dumamar yanayi dinnan sai karuwa yake yi musamman a kasashe masu tasowa irin tamu kasar.

Akwai bukatar samar da hanhoyin rage amfani da gawayi

**BALARABE** Wannan haka yake sani da dama gas hi muna fama da kalubale daban-daban a kasar kada kuma wannan batun shima ya zame mana matsala bayan matsalolin tattalin arziki dake addabarmu.

**SALIS** Kaga dai a tarihin kasashen da suka cigaba sun ke bada gudunmuwa sosai ta hanyoyin samar da iskar gas, amma kuma su ke shan wahalar illar sa.

Samar da yanayi mai kyau na bukatar na bukatar duba irin wannan matsalar don magance ta, daya daga cikin hanyoyin magance ta itace sabbin hanyoyin samar da makamashi kaga kasar mu na da hasken rana da iskamai karfi wadanda za'a iya amfani dasu wajen rage dumamar yanayi.

**BALARABE** Gaskiya ne, sabbin hanyoyin samar da makamashi da hasken lantarki na da mutukar muhimmanci sosai, banda ma rage dumamar yanayi da suke yi, suna samar da guraben aiki ga yan kasa, da habbaka tattalin arzikin kasa.

**SALIS** Mutane su kasance masu tattaunawa akan batu irin wannan a unguwanninsu don samin mafita ta hanyar cimma matsaya na yin amfani da irin wadannan hanyoyi.

**BALARABE** Kwarai kuwa mutanen gari ya kamata su kasance masu tattauna batu irin wannnan a cikin unguwanninsu dan tsara yadda za su koma yin amfani da sabbin hanyoyin samar da hasken lantarki da makamashi sannan kuma a taimaka musu.

**SALIS** Kaga kuwa haka shi zai taimaka wajen komawa ga sabbin hanyoyin, dole **ne mu taimakawa wadanda kila matsalar dumamar yanayi ka iya shafa.**

**BALARABE** Haka ne sani ya kamat a yi hobbasa don gujewa afkawa cikin matsaloli irin na rasa muhalli sabida ambaliyar ruwa ko daukar cututtuka ga ruwan sha da ya gurbata, ko kuma rashin lafiya sakamakon shakar gurbatacciyar iska da sauransu.

Banda amfani da gawayi harkar sufuri wato transportation da harkar noma wato Agriculture suma fa nada irin nasu matsalolin dake haifar da chanjin yanayi.

**SALIS** Kwarai da gaske haka yake Balarabe harkar limi da noma suma na da nasu matsalolin da ke haifar da dumamar yanayi. A bangaren sufuri mutane zasu iaya rugumar tattaki wato tafiya memakon hawa mota ko mashin wadanda injinsu kan dau zafi da fidda hayakin kabon

Sai kuma hawa keke shima zai taimaka sosai.

Sai ta bangaren noma, shuka itatuwa sosai shima zai taimaka sosai.

**BALARABE** Naji dadi sosai da kayi batu akan shuka itatuwa, sabida dazuzzukan mu na fuskantar kalubale na sare itatuwa idan dazuzzukan mu suka dawo yadda suke a da shima hakan zai taimaka wajen yaki da dumamar yanayi.

**SALIS** Kasan fa duk wadannan abubuwan suna bukatar kudi ne wajen aiwatar dasu. Ta yaya zamu sami kudaden yin wannan abubuwan?

**BALARABE** Kasashen da suka ci gaba, suna taimakawa wadanda ke tasowa irin namu da kudade akwai wata gidauniya ta su me suna " The Green Climate Fund" suna taimakawa, sannan mu kuma ya kamat mu hada kai wajen samar da wadansu kudade.

**EPISODE ELEVEN**

**IYABO** Ina jin dadin kasancewa tare da kai, a duk lokacin da muka zauna muna tattaunawa akan yadda wannan garin namu zai cigaba mai dorewa dan yaya da jikokin mu nan gaba.

**SALIS** Naji dadin hakan iyabo, kuma maganar da kikayi kan gina gari hakika yana da kyau. Kinga yadda mutane ke kara yawa a cikin garin ya haifar da cinkoso, da gurbatar yanayi sannan da karancin ababen hawa wanda ba kowa ke samu ba.

Climate justice yana nufin magance irin wadannan matsaloli da aka sansu don tabbatar da cewa kowa ya samu saukin rayuwa.

**IYABO** Wannan haka yake, muna bukatar magance matsalar da harkar sufuri ke haifarwa ta fuskar dumaman yanayi, mu samar da keke da hanyoyin da mutane zasu dinga yin tattataki a kafa.

**SALIS** A'a Iyabo idan aka samar da motoci wadanda kowa zai hau a kaishi inda yake so zai rage batun kowa yace sai ya mallaki motar kashin kansa wanda haka shi ke kawo yawan motoci a garin da yawan zafi da hayakin carbon mai gurbata yanayi.

**IYABO** Gaskiya ne, iska mai kyau da kuma rage cunkoson  gari nada mutukar amfani sosai wajen yin rayuwa mai dadi.

Amma yanzu janyo hankalin mutane dan su chanja yanda suka saba yi a harkokin sufuri zai yi mutukar wuya.

**SALIS** Haka ne, mutane da yawa basa son sabon tsari akan yadda suka saba yi musamman abinda suka saba yi kullum. Akwai bukatar wayarwa da mutane kai ta hanyar sadarwa, da gangami da kuma dan abinda za'a baiwa jama'a, misali cire biyan haraji ga masu motoci da sauransu.

Dole muyi hobbasa domin ganin ba'a  maida wasu al'umma saniyar ware ba wajen samun ci gaba da ababen more rayuwa.

**IYABO** Naji dadin yadda kika kawo wannan batun sabida galibi mutane marasa karfi na shan wahala sosai, hakika tabbatar da jin dadin rayuwarsu ya rataya a wuyanmu.

**SALIS** Banda harkar sufuri, yakamata mu samar da hanyoyi na kawo motoci masu aiki da wuta wadanda za'a dinga chajin su da wuta, sannan mu kawo tsarin yadda za'a rabawa mutane motocin.

Sai dai yana da kyau a fahimci cewa wadannan tsarin ba dare daya ake yinsu ba a hankali- a hankali ake yinsu

Ance ayamun-ayamun matankali kan shiga gora.

Sannan inda duk jirigin sama je a kwana a tashi kunkuru ma zai je, hakuri ne kawai me cidda rabo

## EPISODE TWELVE

**BALA** Bala nayi farin cikin samun wannan dama ta zuwa don muu tattauna batun chanjin yanayi da jibge bola a ko ina.

Kasashe massu tasowa da daman a fama da irin wannan matsalar wadda ke yin tasiri soasai ga dumamar yanayi

**SALIS** Wannan haka yake, gaskiya muhallin mu na fama da irin wannan matsala ta zubda shara ko ina wanda sam hakan bai dace ba. Kyautatawa muhalli shi ne mu kawo karshen wannan matsalar wanda da yawa yana faruwa ne a garuruwa wadanda aka maida su saniyar ware ba'a kulawa da su

**BALA** Hakika jibge bola ko ina na haifar da gurbacewar iska, ya lalata ruwa sannan ya hadddasa cututtka bayan ambaliyar ruwa wanda ya kamata mu rage zubda bola a ko ina ta hanyar yin wuraren zubda ta da kuma kara sarrafata zuwa wani abu daban dan tabbatar da adalci ga kanmu da kuma muhallinmu.

**SALIS** Wannan ba don gujewar haifar da dumamar yanayi ne kadai ba, a'a har da tabbatar da cewa kowa yana iya rayuwa a tsaftataccen wuri, me tsaftataccen ruwan sha da ababen more rayuwa da sauransu.

**BALA** To salis bari mu fara da batun yadda zamu rage zubda shara barkatai musamman yadda muke watsar da robobi da ledoji. Ya kamata muu fara tunanin yadda zamu fara sarrafasu don maida su zuwa wasu abubuwa da muke bukata na amfani.

**SALIS** Ilimi haske ne kuma gishirin zaman duniya ne idan aka ilmantar da mutane kuma aka wayar musu da kai akan illar zubar da shara ko ina kuuma aka wayar masu da kai akan alfanu da ke tattare da muhalli mai tsafta zamuyi nasara kuma mu amfana gaba daya

**BALA** Na yarda da wannan Magana taka, sannan ya zama dole muyi Maganar yadda ya kamata " Yan chabi , ko chibola ke kwashe shara ya kamata a wadata su da kayan aiki ingantattu da zasu kare su daga kamuwa daga cututuka.

**SALIS** Sake sarrafa ledoji da robobi na da mutukar muhimmanci sosai don tsabtace muhalli samar da guraben ayyuka da kuma tattalin aziki

**BALA** Wannan haka yake, salis maganar ka ta bada ma'ana sosai, Climate Justice na nufin yiwa muhalli da mutanen da ke cikisa adalci ta hanyar tabbatar da kowa yarayu a muuhallin da ya dace da ababen more rayuwa sannan da magance matsaloliin muhalli.

**SALIS** Wannan haka yake, to ya maganar fara sarrafa shara ko bola zuwa ga makamashi na samun hasken lantarki da kuma girki.

**BALA** Wannan batun nan kuma zai taimaka wajen magance gurbatar yanayi amma fa sai anyi taka tsan-tsan don gujewa gurbatar iskar da muke shaka da wasu abubuwan da ka iya cutar da al'umma

**SALIS** Haka ne Dakta Bala duk wani abin da za'a yi wajen maida shara zuwa wani abin da za'a iya amfana dole ne  a fi baiwa muhalli da mtanen da ke cikinsa muhimanci ta fuskar lafiyar su da tabbatar da cewa ko wani barayi bai zamo matsala ba.

**BALA** Naji dadi da ka kawo wannan batun, da warware zare da abawa, kayiwa ko wane bangare adalci.

**SALIS** Mutanen kauyuka na da saukin wannan matsalar, dan haka ya kamata su tatauna yadda za'a magance wannan matsala.

**BALA** Yakamata a samar da kayayyakin fasaha na kwashe shara memokon barin bola ta rube a wajen ta gurbata iska sai nau'ura ta sarrafata.

**SALIS** Sabuwar fasahar kwashe shara zata taka rawar gani sosai, amma dole ne a tabbatar da cewa kowa zai iya mallakar na'urori na wannna aikin

## EPISODE THIRTEEN

| | |
|---|---|
| **RABI** | Nayi farin cikin sake haduwar mu yau Salis, don mu kara tattaunawa akan yanayin wanna garin namu. |
| | Adalaci ga muhallinmu da mutanen da ke cikinsa shine bada muhimmaci ga bukatun jama'a musamman wadanda chanjin yanayi ya shafa. |
| SALIS | Matsugunnan da aka ware su akayi watsi da su hakika su ke fuskantar matsalolin chanjn yanayi a koda yaushe. Don haka aikinmu ne tabbatar da cewa sun sami sauki |
| RABI | Mazauna wannan gari na fama da matsalolin ambaliyar ruwa, tsananin zafi da rashin kayayyakin more rayuwa. Yaya garinmu zai habaka ya koma alkarya ? |
| SALIS | Wannab abune babba wato abbar Magana dai a takaice, amma akwai hanyoyin da zamu iya bi don cimma burinm, na farko dai shine mu gina garinmu, mu fitar da hanyoyin ruwa yanda ya dace sannan mu gina benaye dan kaucewa ta'adin ambaliyar ruwa |
| RABI | Wannan haka yake, amma mun sanya mutanen garin cikin dukan tsare-tsaren na gina garin, musamman mutanen da suka fi kowa shiga matsalar irin yanayi wanan. |
| SALIS | Maganarki haka take dole mu hada hannu da mutanen gari kan wannan batu sabida musan irin ababen da suke bukata. |
| RABI | Salis ya batun tsabtataccen ruwan sha da kuma tsabtataccen muhalli? |
| | Wadanda ke haifar da cututtuka lokacin da yanayi yya chanja. |
| SALIS | Ruwa abokin aiki ne kuma abokin rayuwa raywa sai da ruwa a don haka dole ne musamar da hanyoyin samar da tsaftattaccen ruwa ta hanyar samar dda burtsatse na tsakiya r gari da kuma tara ruwan sama da sauransu |

RABI Har na fara ganin kyawon garin a cikin idanuna. Bayan wannan sai batun shara shin ta yaya zamu zamo masu taka tsan-tsan da lamarin da ya shafi shara?

SALIS Idan muka fara sarrafa shara musamman robobi da ledojidon maida su wasu ababen da muke bukata, da maida sharer mu taki ko samar da makamashi hakan zai rage yiwuwar gurbacewar iska da kamuwa da wasu cuttuttuka da ake kamuwa da su ta ruwa ko iska sannan mu sami gari me tsafta.

RABI To ya sabbin hanyoyin samar da hasken lantarki da makamashi?

Mutane da yawa anan suna amfani da tsaffin hanyoyi masu cike da hadari

**SALIS** A gaskiya sabbin hhanyoyin samar da lantarki a makanashi wannan lokaci shine mafita. Misali hasken da solar zai iya samarwa zai iya kancewa a gida koma a gari gaba daya, sannan daga zarar an dauke wuta daga kamfanin lantarki ta kasa shi zai bada haske.

**RABI** Kai amma wannan yayi, kuma shine mafita amma kuma dole mu magance matsalar dai-dai to na karfin tattalin arziki ta hanyar taimakawa mutane da tallafi.

**SALIS** Hakane Rabi, zamu kirkiro wani sabon shiri ko gidauniya ra tallafa wa mutane, sannan mu fio da tsarin rantawa mutane kudi dai-dai misali don kara jarin kasuwancin da suke yi

**RABI** Naji dadin yadda kake abubuwa da zasu magance matsalolin mutanen mu

**SALIS** Adalci ga batun muhalli da chanjin shine taimakwa don magance yadda matsalar yanayi ya shafi muane marasa karfi don tabbatar da cewa mutane na ryuwa mai kyau a inda akwai tsabtataccen ruwan sha iska mai kyau ba waddda ta gurbace ba, muhalli me kyau batare da ambaliya ya kori mutane ya chanja musu matsugunni ba.

**EPISODE FIURTEEN**

SALIS Ina farin cikin sake dawo wa wannan wuri dan sake tattaunawa da ke Rabi, wani kasaitaccen kanti wato SHOPRITE ya kudiri aniyar nuna wa mutane yadda ake tantagaryar aikin gona ba tare da anyiwa muhalli da hallitun da ke rayuwa cikin shi illa ba. Zan so inji cikakken labari yadda abun yake.

RABI Nagode salis naji dadin yadda ka fahimci cewa nasan wani abu game da climate justice da eco- friendly farming. Tabbatar da cewa baa bar kowa a baya ba wajen yin rayuwa a muhalli mai kyau da lafiya shine aikina dan tabbatar da cewar an sami isashen abinci ga Al-umma.

SALIS Karamin haske dai, chanjin yanayi dai a wannan lokacin ya haifar da kalubale da dama a harkar noma, shin wane irin salon aikin noma kike yi ne a halin yanzu

RABI Ina amfani da salon aikin noma ne da Bature ke kira Agro-ecology, wannan irin salon aikin noma shine ba ruwanshi da bukatar wasu sinadarai na Bature a gona ma'ana komi a garagajiyance dan kada a yiwa muhalli illa da abin da ke cikinsa a don haka, ina amfani ne da taki na juji da maganin kwari na gargajiya sabida idan ina yin amfani da maganin kwari na Bature da aka yi da chemical zan iya yiwa muhalli illa

SALI Kai amma wannan salon aikin noma na ki ya burgeni fa, kuma yana karawa kasa danshi da lafiya.

Ta ya kike ganin shoprite zai taimakama manoma kamarki don bunkasa irin wannan salon aikin noma?

RABI Idan aka hada kai da manoma irina don samun bayanai da kayan gona a wajen mu komi komi zai kai ga Jama'a ta hanyar kasuwanci da shoprite din keyi hakan zai baiwa sauran manoma kwarin gwuiwar fara irin wannan salon aikin noma

SALIS Wannan haka yake, amma kuma wannan batu ne na ilmantar da mutane da wayar masu da kai akan irin wannan tsarin noma ,shin ya kike ganin za'a wayarwa da mutane kai don gane muhimmancin irin wannan salon noma naki?

RABI Hakika ilmantar da mutane kan wannan shi ya fi dacewa, sannan yan kasuwa zasu iya hada guiwa da mu manoma a kuma shirya tarurrukan karawa juna sani, da gangami kai har ma da shela akan wannan batu. Idan mutane suka ga haka abu shakka hankalinsu zai karkata zuwa ga wannna tsarin.

SALIS Hakika na gamsu da irin wannan bayani naki, kawo yanzu wadansu irin kalubale ne kike fuskanta wajen aiwatar a irin wannan aikin noma?

RABI Gakiya akwai matsaloli, kaga dai na farko shi ne matsalar kudi da kayan aiki na zamani wadand su ne matsalolin kananan manoma irina.

Hada guiwa da yan kasuwa, da kungiyoyi da kamfani masu zaman kansu da wakilan gwamnati zai taimawa kananan maonoma irina kaga bama samun haka musamman ni dai.

SALIS Naji dadi da kika yi maganar hadin guiwa a gaskiya hadin guiwa da ma su ruwa da tsaki zai kai harkar noma ga nasara. Bari muyi maganar tattalin arziki, ya zaki bayyana irin kudi ko ribar da kike samu ta amfani da irin wannan salo na aikin noma?

RABI Da farko dai da na fara akwai yan matsaloli nan da can amma yanzu da na fahimta ba karamin kudi nake samu ba  akwai riba.

SALIS Masha Allah! Wannan shine abu mai muuhimmanci na taya ki murna. Aikin noma wanda akayi nasara shi ne wanda akayi shi aka samu nasara sannan kasar nom aba ta gurbata ba tana da kimarta .

RABI Wannan bayun haka yake, muna bukatar riba amma a tabbatar riba ta samu ta ba tare da lalata kasar noma ba. Wannan shine adalci ga muhalli da irin halittun da ke rayuwa a cikinsa.

**EPISODE FIFTEEN**

**SALI** Barka da zuwa wannan wuri Aliyu, matsalar dumamar yanayi matsala ce da ta shafi kasahse masu tasowa irin namu wadanda ke da hannu kadan wajen haifar da shi

**ALIYU** Salis barka da warhaka, naji dadin kawo wannan maudu'in da kayina chanjin yanayi da farko dai bankin habbaka Nigeria, wato Developemennt Bank of Nigeria mun kudiri aniiyar magance matsalar chanjin yanayi da kawo ci gaba mai dorewa.

**SALIS** Adalci ga muhalli da mazauna cikinsa shine a baiwa kowa hakkinsa na rayuwa ba tare da nuna fifiko ga wani bangare ba, ma'ana idan dadi ya zo a ji dadin rayuwa tare, haka idan ibtala'I ta fadawa mutane a magance ta ba tare da an ware su ba musamman wadanda basu da kudi da abubuwa na zamani dan sajewa da da chnjin yanayi da suka tsinci kawunan su a cik.

Kasashen da suka ci gaba a duniya wato kasashen ketare sun lashi takobin daidaita mutane ba tare da nuna fifiko ba.

ALIYU Muna sane da muhimmancin daidaita mutane da matsalar chanjin yanayi ya shafa sannan muna yin mai yiwuwa don tabbatar da cewa sunyi rayuwa mai kyau kamar kowa,. To aamma kui sunyi wahala a halin yanzu ta yaya kake ganin zau samar da isashen kudi ga kasashe kamar Niigeria?

SALIS Kudi shine babban abin da za'a iya kashse masu tasowa da su don ta fida irin chanjin yanayin da ya riskesu don rage radadin illar da chanjin yanayi musu kuma su saba da yanayin.

Amma yana manyan kasashen da suka cigaba su cika alkawarin da sukayi na taimakawa da kudade ga kasashe masu tasowa.

Yana da kyau mu marawa wannan batu baya don a dinga samun kudade daga kasashen ketare don don samin cigaba mai dorewa.

ALIYU — Lalle ka kawo haske sosai cikin wannan lamari kasashen da suka ci gaba suna da irin rawar da zasu taka sosai. To amma  me kake ganin ya kamat ta bangaren mu muyi a matsayin mu nay an kasa?

SALIS — Tsare-tsare na da muhimmanci sosai, ya kamata gwamnati ta kawo sabbin tsare-tsare na aikin noma da samar da ruwa, da gina kasa sannan ta karawa yan kasa  kwarin guiwar amfani da sabbin hanyoyin samar da hasken lantarki da makamashi da amfani da kasar noma yadda ya dace, idan akayi haka zai taimaka wajen samin sauki na chanjin yanayi

ALIYU — Kai amma wannan shawara taka fa tayi sosai muna goyon bayan wadannan abubuwan amma kalubalen cin hanci da rashawa da rashin wayar da kan al'umma yana hana irin wannan tasiri. Ta ya za'a wayarwa jama'a kai?

SALIS — Magance cin hanci da rashawa fa da wayar wa Jama'a kai ba karamin al'amari ne ba,amma idan gwamnati zata bayyana komi ga jama'a sannan ta  janyo mutane da abin ya shafa komi a yi tare da su hakan zai dakile batun cin hanci da rashawa a cikin lamarin.  Bayan haka sai ilmantar da mutane ta hanyoyi da dama za'a sami nasara.

ALIYU — Gaskiya naji dadin wadannan bayanai daga gareka kuma na karu.

Kuma na fahimci hada kai da manoma da bankuna zai kai ga samun nasarar magance matsalar sauyin yanayi. Na gode

SALIS — Nima na gode kwarai da gaske.

**EPISODE SIXTEEN**

SALIS Ina maka lale marhabin, barka da samun lokacin zuwa don mu tattauna akan matsalar da ta shafirayuwar duk fadin duniya, wannan ba wata matsala ba ce illa matsalar chanjin yanayi da yadda samar da kudade za su magance matsalar, sunanan Salis.

ALIYU Yauwa Salis barka da warhaka, naji dadin kawo wannan batun da kayi, kuma ba karya bane chanjin yanayi matsala ce da t addabi fadin duniy baki daya. A matsayin mu na mataimakan Bankin habbaka kasa,mun duba wasu ayyuka don magance matsalar lamari na chanjin yanayi.

SALIS Masha Allah! Naji dadi da ka fadi cewa adalci ga muhalli da mazauna cikinsa shine gane cewa asalin ababen dake kawo dumamar yanayi mafi akasarinsu daga kasashen ketare wadanda suka ci gaba amma kuma mu ke shan wahalarsa a kasashe masu tasowa irin namu.

Shin ta yaya zamu tabbatar da cewa nauyin dawainiyar magance matsalar an rabashi daidai ba'a cuce mu ba?

ALIYU Gaskiya kayi Magana a nan, Climate justice na nufin samar wa mutane wadanda basu ji ba su gani ba wajen haifar da dumamar yanayi mafita ta hanyar samar masu da kudade don samun sauki wajen tafiya da sabon yanayi da suka tsinci kawunan su a cik. Wadanan kudade da za'a samar daga Development Bank, da su ne za'a samar wa mutane da sauyin yanayi yayi wa illa matsugunni mai kyau, kayan aikin noma na zamani da gina gari da sauransu.

Development Bank na taka muhimmiyar rawa a wannan lamari.

SALIS Kai amma fa naji dadin wannan bayani, to ammma fa sai dai akwai babban kalubale wajen bada wannan kudade a kasashe masu tasowa dan bas u ko zasu bada zaka gad an abin da zasu bayar ba zai yi komi ba.

Abin tambaya anan shine ta ya Development Bank zata tabbatar da cewa ta bada kudade isassu dan tunkarar wannan matsala?

ALIYU Gaskiya ne, samar da kudade irin wannan nada wahala, amma Development Bank of Nigeria tana yin mai yiwuwa dan fara bada rance ga Al'umma da chanjin yanayi ya shafa muna aiki tukuru da kungiyoyin daga kasashen waje don tabbatar da wannan tsarin.

SALIS Hakika Wannan abu yayi daidai, bugu da kari idan ma har za'a yi adalci wajen bada kudin da bin diddigin yadda aka kasha su, hakan nada mutukar amfani , abin tambaya a nan shi ne ta yaya za'a tabbatar da cewa kudaden da aka ba al'umma ya kai garesu sannan anyi amfani da kudin yadda ya kamata>

ALIYU Tsarin mu na tafiya bai daya da mutanen gari zai taimaka sannan muna da kudirori guda ukku na farko shine zaben inda zamu yiwa aiki, sai na biyu aiwatar da aikin, na karshe shi ne dubawa da bin diddigin aikin, kaga wannan ai ba sai an gaya wa mutum ba Insaha Allahu za'a sami nasara

SALIS Sanya mutanen gari tsundum cikin lamarin yin wannan aikin yanada muhimmanci sosai ya development Bank of Nigeria zai bada zai bada kudi masu kia dan magance matsalar chanjin yanayi?

ALIYU Muna hada karfi ne da karfe dan cimma wannan buri namu, Ma'ana muna hada hannu ne da manyan kasashen duniya da suka ci gaba don samar da kudade ga al'umma.

SALIS Naji dadin wannan zantawa da mukayi na gode duk da cewa ina da tambayoyi da yawa amma

**EPISODE SEVENTEEN**

**SALIS** Ina farin cikin kara kasancewa tare da ke, don zantawa akan muhimmin abu irin wanna wato ilimin chanjin yanayi a kashashen mu masu tasowa. Baraka da zuwa Rabi.

**RABI** Yauwa barkan ka dai Salis nag ode sosai da ka bani wannan dama, Ni ke wakiltar makarntar mu kan wannan batun na ilimin chanjin yanayi na ilimin chanjin yanayi a kasashe masu tasowa wanda zamu tattauna akai.

**SALIS** Da farko dai idan bature ya ce climate justice yana nufin cewa yadda zaa tabbatar an magance matsalar chanjin yanayi da yayi wa wani bangare na mutane dai-dai wa daida ba tare da an nuna wani fifiko ga wani bangare ba ta hanyar tabbatar da cewa mutane sun rayua muhalli mai tsafta, ruwan sha mai tsafta da koren muhalli mai lafiyayar iska ba gurbatacciy ba da dai suransu.

illar chanjin yanayi ya fi damun kasashe masu tasowa shin ya makarantu ke taimakawa don magance wannan matsalar a bangaren ilimi ?

RABI Nagode, Da farko dai makarantarmu ta shirya tsaf don sanya ilimin chanjin yanayi cikin manhajar karatu don ilmantar da dalibai, daliban mu zasu koyi ilimin kimiyya da ya shafi yanayi, mun kuma shirya taron karawa juna sani da gangami da kuma sauransu

SALIS Ba shakka! Da alama kun shirya sosai na ji dadin wanna batu, ilimin yanayi ban a dalibai ne kadai ba ilimi ne da ya kamat a ce kowa yana dashi.

Ta yaya ,akarntarku zata fadada wannan ilimi zuwa makwabta da sauran jama’a?

RABI Muna kokari hada hannu da kungiyoyi masu zaman kansu dake wannan gari da masana’antu masu zaman kansu da mai’katun gwamnati don

tsara shirye shirye na wayar wa mutane kai akan chanjin yanayi, musamman irin illar da ya kewa al'ummar da aka maida ta saniyar ware da sauransu

SALIS Wannan gaskiya ne, sanya mutanen gari tsundum cikin wannan lamari zai kawo nasarar abin. Ta ya wannan ilimi zai kai ga mutanen da ba'a yi tsammani zai kai gare su ba?

RABI Zamu hada kai ne da hukumar wannan gari don yin tsarin karatarwa tafi da gidanka zuwa wadannan wurare, sannan zamu bada tallafi da Scholership ga dalibai don su karo ilimin abin musamman daliban da suka fito daga godajen marasa karfi.

SALIS Shin ya makarantarku zata baiwa dalibai kaunar hanyoyin maganin matsalar chanjin yanayi?

RABI Daliban mu tuni sun kasance cikin kungiyar rajin kare muhalli dake cikin makarantar mu, suna san club din sosai sannan muna basu kwarin guiwa shiga Ayyukan sa kai na cikin unguwa, sannan mukanyi gangami dan nuna musu yadda abin ke tasiri ga Jama'a

SALIS Masha Allah! Wane abu makarantarku ke da burin yi nan gaba kan ilimin chanjin yanayi?

RABI Burinmu shine mu samar da dalibi masu ilimi da hazaka, kuma yan kasa na gari sannan mun lashi takobin ganin cewa mun yi amfani dailimin da allah ya bamu do magance matsalar chanjin yanayi

SALIS Hakika kana da buri mai kyau sai dai mu yi maku fatan alkhairi. Mun gode malama Rabi.

RABI A madadin Malamai da Dalibai da hukumar Makarantar mu muma mun gode kwarai da gaske.

**EPISODE EIGHTEEN**

**SALIS** Ina yi wa kowa barka da isowa wannan wuri don tattaunawa akan Babbar matsalar dda ta addabi kasarmu, wato afkowar dumamar yanayi wanda ya haifar da chanjin yanayi da yadda zamu yi don rage hadarin da illar ke haifarwa irin na Ambaliyar ruwa, rasa matsugunai, kamuwa da cututtuka irinsu kwalara da gurbacewr iska da muhalli da dai sauransu, sunana Salis

**RABI** Ina yiwa kowa barka da zuwa wannan wuri, hakika chanjin yanayi ya haifar da karuwar kunci musmamn ga mutanen da aka maida su saniyar ware, yana da kyau muyi maganin wannan kalubalen ba tare da bata lokaci ba.

**ALIYU** Wannan gaskiya ne, hakika chanjin yanayi ya haifar da bala'i ga Al'ummar mu. Ya kamata muyi rigakafin kare mutanen da wannan bala'i ke shafa.

**IYABO** Ina godiya da samun damar da aka bani don wakiltar al'umar mu. A gaskiya mun dandani irin wahalar da chanjin yanayi ke kawowa abin dai babu dadi. Lokaci yayi da zamu yi aiki tare wajen yin maganin akuwar wannan bala'i

**SALIS** Hakika gwamnati na yin dukkan mai yiwuwa don show kan wannan lamarin, muna aiki tukuuru wajen tsara yadda za'a yi wannan aiki ina nufin mutanen da matsalar dumamar yanayi ya shafe su don ganin cewa sun yi rayuwa a garuruwan su kamar kowa ba tare da bambanci ba.

**RABI** Bugu da kari, kudin d aka ware don taimakawa irin wadannan mutane yana da mutukar muhimmanc. Akwai bukatar isashen kudi don gudanar da ayyukan taimakawa wadanda iftil'in ya shafa, bayan haka akwai bukatar bin diddigi don tabbatr da cewa kudaden da za'a baiwa Al'umma sun kai gare su.

**ALIYU** Aiwatar da komi a bayyane da amana suna da mutukar muuhimmanci wajen aiwatar wannan aiki na agaji ga mutane.

Dole mu bada dokoki, na yadda za'a tafiyar da kudaden

IYABO Kada mu manta da tsarawa da gina gari mai tsafta sannan da samar da kimiyar gargadin faruwar iftila'I da ka iya afakawa alumma, don rage yawan asara da za'a iya samu

SALIS Gina gari da habbaka shi ta yadda mutane zasu yi rayuwa me kyau na daga cikin ababen da za mu ba fifiko, muna hada guiwa da kungiyoyi daga kasashen waje don cimma wannan burin.

RABI Gaskiya abin farin ciki ne idan wannan ya tabbata, amma tabbatar da an baiwa maza da mata komi dai-dai a fita hakkin kowa sabida bala'I ba ta tantance kowa take shafa idan tazo kuma mata sun fi shan wahala.

ALIYU Wannan haka yake, ya kamata a duba wannan batu

SALIS Ina godiya gare ku duka da samin damar halartar wannan wuri.

**EPISODE NINTEEN**

**SALIS** Ina yiwa kowa barka da zuwa wannan dakin taro don samo mafita kan yadda Dumamar yanayi da ke haifar da chanjin yanayi ke zama ummul aba'isi wajen gurbata iskar da mu ke shaka yau da kullum a kasahse masu tasowa wato Developing countries a turance.

**RABI** Barkanmu da warhaka, Gurbacewar iska abin damuwa ne mutuka ga lafiyar mu musamman a garuruwan mu da keda cinkoson jama'a. Yana da kyau muyi kokarin magance wannan matsalar.

IYABO Kwarai da gaske kuwa, adalci ga muhalli shi ne tabbatar da cewa dukkan mutane a kowane gari sun rayu da tsaftataccen muhalli da iska me kyau sannan da ruwan sha mai kayu da sauransu.

ALIYU Eh to a ganina tsara gina gari nada mutukar muhimmanci idan har ana so a sami iska mai kyau. Sannan akwai bukatar sabbin dokoki a harkar sufuri, da batun itatuwa sannan da yadda ake zubda shara.

SALIS Kayi Magana me ma'ana, Gwamnatinmu na kokarin yin dokoki musamman ga masana'antu da ababen hawa kan gurbata muhalli ta iskar da muke shaka yau da kullum. Da wayar wa mutane kai akan sabbin hanyoyin hasken lantarki da makamshi, don rage dumamar yanayi.

RABI Wannan haka yake gurbatacciyar iska na kawo matsalr numfashi

IYABO Kada a manta da yin aiki kafad-da kafada da yan asalin gari, kun san Hausawa na cewa "me daki shi yasan inda yake masa yoyo" idan aka tafi da mutanen gari hakan zai kara musu karfin guiwa kuma za'a sami nasara don zasu dinga sa ido akan dukkan abubuwan da za'a yi

ALIYU Yin aiki kafada da- kafada da mutanen gari zai zai samar da mafita a yunkurin mu na aikin tsara biran, sa'annan da yan gari masu ruwa da tsaki don samun nasara habbaka gari mai lafiyayyar iska da lafiyar mutane

SALIS Hakika na yadda da wannan Magana taku dari – biasa dari, shima fa ilmantar da mutane akan muhalli da yanayi wani abu ne da ya kamata mu baiwa muhimmanci, ta hanyar wayar wa mutane kai akan dangantakar Climate Justice da gurbatacciya iska kogurbataccen muhalli.

RABI Ilimi haske ne, akwai bukatar koyar da mutane yadda zasu rage amfani da wasu ababe masu haifar da dumamar yanayi,don su koma yin su koma yin amfani da abubuwan da suka dace da muuhallin mu

IYABO Bayan wadannan ya kamata mu kawo karshen gurbata ciki gidajenmu, mutane da ywa sun fi gane yin amfani da itace ko kanamzir a cikin gidajensu, kuma suna amfani da fitila mai amfani da kalanzir don ganin haske kuma yana da hadari mutuka ga lafiyarmu ya kamata kowa ya mallaki wadannan abubuwa na zamani da za su sauya wadancan

SALIS Iskar da yakamata mu dinga shaka a cikin gida na da da mutukar amfani galafiyar mu gwamnatin mu nayin dukka mai yiwuwa wajen samar da sabbin hanyoyin samar da hasken lantarki da makamashi da yan kudi kalilan. Wanda kowa zai iya mallaka.

ALIYU Haka ne bayan wadannan yana da kyau mu dauki halin shuka itatuwa a biranen mu sannan dukkan tazara tsakanin gini da gini ya kasance kore shar da shuke-shuken fulawoyi da tabarmar ciyawa da sauransu

RABI Wurare irin wadannan nada mutukar amfani ga lafiyar mu

IYABO Daga karshe a tabbatar da an kamata adalci wajen tsare-tsaren yi ayyukan da aiwatar dasu

SALIS Adalci shi muka sanya a gaba don ganin cewa an baiwa mabukata agaji da taimaka musu

**EPISODE TWENTY**

| | |
|---|---|
| SALIS | Jama'a lale marhabin da sake taruwa a wannan azure. Yau ma Allah yayi wai aure da mara kwabo, yau ma gashi mun sake zama dan zantawa akan yanayin mu wanda hakika ya chanja sannan da muhallin mu wanda ke cike da jama'a da kasar noma, kana da hallitu wadanda me ke iya gani da wadanda ma bama iya gani a kasashen mu masu tasowa. Har la yau barkan ku da zuwa. |
| RABI | Yauwa Salis mun gode kwarai da gaske muhallin mu wanda ke cike da jama'a da halittu da daman a da mutukar muhimmanci a gare mu kuma shine kashin bayan rayuwar mu. Kokari kare muhallin mu na tabbattar da rayuwa na tabbabtar da rayuwa me kyau a muhallin mu. |
| IYABO | Iyaye da kakanni mu sun tattala muhallin mu shekaru aru-aru. Duk wani abu da za'a tsara game da muhallin mu ya kasance ya mutunta yadda kakannin mu suka rayu a cikinsa. |
| ALIYU | Na yarda da wannan batun kungiyiyi masu zaman kansu ma na taka muhimmiyar rawa wajen tatalin muhallin mu, da kokarin ganin cewa mutane sun yi rayuwa me kyau. |
| SALIS | Gwamnati na kokari sosai wajen tabbatar da cewa an sami dai-daito ta fuskar rayuwa me kyau |
| RABI | Idan muhalli ya rasa wadansu hallittu ko ababe da ke tare da shi, mutane kan ji a jkinsu |
| IYABO | Wannan gaskiya ne, al'ummr mu na tafiya dda muuhalli ya taimaka sosai wajen tabbatar da muhalli me kyau shekara da shekaru |
| ALIYU | Samar da kudin aiki shi ne babban Kalubale, amma kungiyoyi masu zaman kansu zasu taimaka sosai wajen samar da kudade don yin ayyuka da |

wayarwa jama'a kai don sanin muhimmancin samar da muhalli ga wadanda matsalar chanjin yanayi ya shafa

| | |
|---|---|
| SALIS | Wannan haka yake, zamu hada guiwa da kungiyoyin kasashen waje don samar da kudade da bunkasa harkar yawon shakatawa |
| RABI | Hakika idan wannan ya tabbata muhalli zai inganta. |
| IYABO | A matsayin mu nay an kasa muna da horo na al'adun mu, dole mu tabbatar da harkar yawon bude ido a kasar mu be taba al'adunmu ba. |
| ALIYU | Al'adun mu na da mutukar muhimmanci, kungiyoyi masu zaman kansu za su taimaka wajen samarwa ko tsara ko tsara shirye-shirye don ilmantar da kan jama'a kan wannan. |
| SALIS | Wannan haka yake, zamu tabbatar da cewa duk wani aiki da za'a yi na gyara gari bai tsaya a irin yadda Bature ya tsara kawai ba, ya tafi daidai da al'adun mu na gargajiya. |
| RABI | Kada a manta da matasa wajen bada wannan ilimi, ya kamata su sami ilimin abin sosai |
| SALIS | Godiya gareku duka fatan kowa zai koma lafiya sai anjima |

## EPISODE TWENTY ONE

## SHAWO KAN MATSALAR TARI DA AMBALIYAR RUWA DON RAYUWA MAI DOREWA

Acikin yan shekarun nan duniya ta dandan wani irin yanayi mai radadi wanda ba'bagani ba saba gani ba a yan shekarun baya, kuma daga yanayi na Bala'in ambaliyar ruwa da kuma fari harma da kamfan ruwa wannan nada nasaba ne da dumamar yanayi, wanda haka ya zamo kaul-bale ga ilahirin kasashe da Al'ummar Duniya

A wannan shirin namu za muji yadda dangantaka take tsakanin ambaliyar ruwa da fari da kuma yadda za'a magance matsalar.

## INTERLUDE

Madallah!

Da ambaliyar ruwa da fari Dan juma ne da dan jummai ta fuskar haifar da matsala ga Bil'adama.

Aukuwar sun a faruwa ne bayan daya yazo yayi ta'adi ya tafi sai daya ya zo a bayansa.

Misali idan ruwan sama ya sauka kamar da bakin kwarya, sai ya haifar da ambaliya, da zarar an wanye ga ambaliyar kuma sai fari ya biyo baya ko kamfan ruwa. A don haka yana da kyau a lakanci irin wannan yanayin don magance shit hanyar yi ma kyawawan shiri kamar haka:

1. Ya kamata a yi habbasa wajen tattara ruwa da sanin yadda yake zuwa ya kare, wato daga lokacin da damina ke faraway da karshenta.
2. A tabbatar da ba'a barnatar da tsirrai da halittun da ke gandun dazuzzukan mu, musamman itatuwa a kiyayi sare su dan suna tainakawa ta fuskar samar da danshi a lokacin fari, da rage karfin iiska da ambaliya.
3. A tabbatr da ana tara ruwan sama a manya tankoki a lokaci damina, irin wannan ruwan zai yi amfani mutuka wajen ban ruwa a lokacin fari.
4. Kada a dinga dogara da hanyar samar wa yabanya ruwa daya tilo sabida yin hakan ragon azanci ne.
5. Sannan ya kamata a ilimantar da mutane a unguwanni ta yadda za'a hada karfi da karfe ta yadda za'a magance wannan matsala kana ayi tsari ko dokoki ta bangaren

gwamnatina yadda mutane zasu kaucewa abubuwan da ke haifar da ambaliyar ruwa, sannan hukumar da ke kula da bangaren ruwa da tattalinsa ta shigo cikin lamarin.

Daga karshe gwamnati da kungiyoyi masu zaman kansu dole su yi aiki bai daya don samar da mafita.

Hakika magance matsalar ambaliyar ruwa da fari na bukatar abubuwa da dama don ba karamin aiki bane, a don haka dole ne kowa da kowa ya bada gudun muwa don tunkarar kalu-bale

**EPISODE TWENTY TWO**

**RASHIN ADALCI GA WANDA IFTILA'I NA FARI KO AMBALIYAR**

A cikin yan shekarun nan dunya ta farga daga yadda aka maida wasu rukunin jama'a saniyar ware, wato mutanen da basa samun ingatacciyar rayuwa kamar sauran mutane yan uwansu.

Mutanen da dumamar yanayi yayi wa illa ta hanyar ambaliyar ruwa kan rasa ko mi har da matsuguninsu irin wadannan mutane bas safai suke samun dauki daga gwamnati ko kungiyoyi ko wasu hukumomi an maida su saniyar ware, basu da ruwan sha mai tsafta basu da ingantacciyar iska shaka sabida gurbatar yanayi, babu wajen kwana da hasken wutar lantarki, babu hanyoyinn sufuri ma su inganci. Hukumomi a nahiyar mu ta Africa su fi maida hankali ne kawai akan yadda wawushe asusun kasa da gina kawunansu. Maimakon lalubo hanyoyin magance matsalar dumamar yanayi zamu duba wannan batu don ganin yadda zai zamo matsala a nahiyar mu ta Africa da Duniya baki daya.

**INTERLUDE**

Madallah!

Wawushe asusun gwamnati ko kasa na nufin sace kudi don azurta kai ta hanyar haramun.

Wannan lamari na kawowa kasashen mu na Africa koma bay aba kadan ba, ta fuskoki da dama cikinsu hadda muhallinmu wanda alal hakika halin ko in kula ya sanya muhallinmu ya gurbace

Kasashen muu na Africa na fama da matsalar dumamar yanayi duk kuwa da cewa ba kasashen ne ke da alhakin haddasa dumamar yanayin ba.

Barnatar da dukiyar kasa ta hanyar wawushe su ya taimaka wajen kasa magance matsalolin dumamar yanayi wanada ke da bukatar kudi sosai da magance shi wanda kuma hakan ya sanya matsalar taki ci –taki cin yewa sabida rashin kudade da kayan aiki

Misali, hako danyen mai da ake yi da wasu ma'adanai akwai rashawa cikin lamarin da kuma kin biyan haraji.

Ribar da ya kamat a samu dan amfanar da yan kasa an karkatar da su zuwa wadansu kassashe an bar al'umma da bakar talauci da da lalcewar muhalli

Wannan ba karamin illah ya keyiwa kasa da mutananta ba a daya bangaren ya karawa tattalin arzikin wadancan kasashen karfi, ya barmu da wahala na tattaalin arziki, matsalolin dumamar yanayi gurbata muhalli  da maida wadansu yan kasa saniyar ware.

Shin me ya kamata mu fara yi a dai-dai wannan lokacin dan fara yi dan samun sauki?

1. Ya kamata a dinga kididigar kudi, ma'ana a dinga binkadin yadda  aka kashe kudi don gano inda akayi rub da ciki da kudaden kasa a  cikin kasa da wajenta, sa'annan bayyana kadarori na ma'aikatan gwamnati da yan siyasa.
2. Sannan ya kamata duniy da hada kai ta hanyar yarjejeniya don kwatowa da maidowa kasa abinda aka sata a cikin ta.
3. Daga karshe a tabbtar da cewa kudaden da aka kwato na sata daga kasashen ke tare anyi amfani da su yadda ya dace

   Magance matsalar barnatr da kudaden kasa da wawuresu wani mataki ne na samar da kudade dan yiwa al'ummar kasa da aka maida saniyar ware ayyuka dan sama masu ababen more rayuwa kamar kowa, da kuma magance matsalolin dumamar yanayi.

   Idan muhka fahimci illolin da sace kudade sukeyi a kasashen mu na Africa ana kais u wasu kasashe da suka ci gaba ke yi kasashen mu zamuyi habbasa dan ganin cewa mun dakile wannan mummunar lamari don ciyar da kasahsen mu gaba.

## EPISODE TWENTY THREE

## YAWAN BASUKAN KASASHEN AFRICA DA KASA YIN KATABUS GA MUTANEN DA CHANJIN YANAYI YA SAHFA

Matsalar dumamar yanayi ba wai ya tsaya ne akan matsalar muhalli kadai bay a shafi tattalin arzikin kasa da  rayuwar yau da kullum na Jama'a.

Ga shi nan ma a zahiri matsalar a nahiyar mu ta Africa wadanda matsalar ta haifar da ciwo bashi ga kasashen namu na Africa.

Bari mu duba yanda nauyin basuka da kuma irin ayyukan da ya kamata a ce an yiwa mutane da basa iya rayuwa na jin dadikamar kowa musamman mutanen da dumamar yanayi ya shafe su.

### INTERLUDE

Nahiyar Africa na daya daga cikin nahiyoyin da matsalar dumamar yanayi ya addaba, duk da cewa gudunmuwar mu kalilan ne na haifar da wannan matsala amma mu ke fama da ambaiyar ruwa, fari da kamfar ruwa da talauci wanda ke dagula mana lissafi.

Kasashen Africa da dama sun ciwo bashi daga kasashen da suka ci gaba a duniya sabida dalilai daban-daban wadanda suka hada da gina kasa da habbaka tattatlin arziki da sauransu wanda kuma wadannan basuka  na lakume wani bangare na kasafi kudi da kasa kan yi ta bar kadan.

Wannana irin bashi hakika yana karawa kasa talauci don yana hana tattalin arzikin kasa habaka wanda kuma kan sanya kasar da ta ciwo bashi ta kasa cimma yarjejeniyar da akayi da iita a sa'ilin karban bashin a don haka biyan bashin kawo tarnaki wajen maida hankali don magance matsalolin dumamar yanayi da ya afkawwa kasa.

Misali, kashashe irin su Nigeria da Angola a Africa, kasashhe ne da ke da tatttalin arziki amma suna da tarun basuka akansu sannan kuma a dayan bangaren suna fama da matsalar chanji yanayi wanda bashi da tabbas.

Irin yarjejeniya da akayi da kasa kafn a bata bashi yana da dan Karen wahala inda kasashenmu su cika wannan sharuddan yarjejejniyar a don haka basa iya magance matsalolin da dumamar yanayi ya haifar a kasashen su.

A takaice dai wadansu hanyoyi da za’a iya bi don magance wannan matsala:

1. Na farko dai yaka mata a canja tsarin yadda ake bada wannan rance don kasa ta samu damar samun wannan kudaden da zata iya tunkarar matsalar hanjin yanayi
2. Na biyu kasashen Africa su nemo wata hanya daban da zasu iya samarwa kasashensu kudi ba sai ta wannan kasashen da suka ci gaba ba.
3. A kirikiro wata fasaha na yadda za’a sami goyon baya wajen magance wannan matsal.

   Sannan ya kamata kasashen ketare su san hakkin da ya rataya a wuyansu na magance matsalolin chanjin yanayi.

   Samun nasarar wannan nahiyar ta mu ta Africa ba wai aikin mutum daya bane, aiki ne da ya rataya a wuyan kowa da kowa sannan yana da kyau mu sani cewa wannan baban kalu—bale ne a gare mu.

**EPISODE TWENTY FOUR**

**DAGA PARIS ZUWA GLASGOW ANA HADA HANNU DON SHAWO KAN MATSALAR DUMAMAR YANAYI**

Matsalar dumamar yanayi ,atsala ce da shafi kowa a duniya. A don haka ne ma kasashe ke taruwa don magance wannan matsalata dumamar yanayi. Wannan irin taro shine na farko na yadda kasashe zasu fara daukar mataki

A wnanna zamu duba irin wannan taro da kuma matakin da aka kai a yunkurin magance wannan matsalar. Musamman a taro na shekarun baya da yya wakana a Paris.

**INTERLUDE**

Madallah!

Taron da ya gudana a paris a shekarar 2015 yayi mutukar tasiri na hada kan kasashen duniya kusa kasashe 200, wanda ko wace kasa na yadda ta dukufa don magance matsalr dumamar yanayi ta hanyar rage yada tururi da zafi da na'urori na ma'aikatu ke fidda wa.

Taron ya duba da kuma yin la'akari da kasashen da suka ci gaba a duniya wadanda kuma suke da hannu dumu-dumu wajen haifar da wannan matsala ta dumamar yanayi da yadda ko wace kasa za ta bada gudun mawa.

Shin kun san ma'anar COP a turance ? COP na nufin Conference of the Parties, wato taro da kasashen da ke cikin majalissar dinkin duniya kan yi wanda ake kira COP 26. Irin wannan taro na baya- bayan nan ya wakana ne Glasgow a shekarar 2021. Makasudin taron shine don hanzarta rage dumamar yanayi zuwa 1.5 na ma'aunin Celcus, sannan sa'annan kasashe su duba Inda aka sami nasara a kokarin magance matsalar da kuma inda za'a dora don gani cewa matsalar ta kau gaba daya, sannan ta samar da sabbin tsare-tsare.

A taron COP26 na 2023 da ya gudana a Glasgow an cimma matsaya kamar haka:

Na farko bada gudun muwa da kasashe zasu yi musamman kasashen da suka fi haifarwa da kuma samar da zafi dake haddasa dumamar yanayi irin su china da Amuruka.

Sai na biyu kasashe dari sun amince kan da rage fitar da sinadarin Methene da kasha 30

Sannan kasashe sun sha alwashin dawo da martabar gandun daji a kasashen da ake yawan sare itatuwa da kin shuka su

Kalubalen da COP ke fuskanta shi ne na wadansu da ke sace dukiyar kasa su barnata kudaden ba tar da yin komi dan magance dumamar yanayi ba.

Kungiyoyi fararen hula da yan gwagwarmaya suna kokari mutuka na magance wannan matsala, suna matsin lamba ga gwamnati don ganin cewa gwamnati ta tyi wani abu.